
# NAUYIN



# ZUNUBI

**Ni, mutumin gabas ta tsakiya ne,** a kullum na kan ji dadin tattaunawa da abokaina a wannan bangare na duniya. Wata rana, na ce masu, ko kun san cewa mutane da yawa sun yi imani cewa, a rana ta karshe, Allah zai auna ayyukansu masu kyau a ma'auni a wannan hannun, ayyukansu na mugunta kuma a daya hannun, wanda ta haka zai nuna za su shiga (sama) aljanna ko kuma jahannama? Sai suka amsa suka ce, I, haka ne, amma kai fa, ba ka yi tunanin hakan ba? Na yi shiru, na dan wani lokaci, daga nan, sai na amsa cewa, tun da mutane da yawa sun yi imanin haka, wannan ya sa na yi tunani mai zurfi, cewa, idan na sami dukan duniya, amma a karshe na rasa raina ina amfanin wannan? Amma bisa ga yawan tunanin da nake yi akan wannan, yawan damuwar da takan zo mini. Sai suka ce, me kake nufi? Sai na ce, to, idan Allah zai sa zunubaina akan ma'auni zan so in san nauyin kowanne zunubina, ku fa? Zan so in san nauyin kowace karya, da mugun tunani da kuma girman kaina. Fiye da komai ma, zan so in san nauyin dukan zunubaina a gaban Allah Mai Tsarki wanda ba ya son zunubi. Ba shi kenan ba. Zan yi mamakin nauyin ayyukana masu kyau, ganin cewa sun kasa domin suna cike da girman kai da lalata, da son neman yabo daga mutane.

**Abokaina sun yi shiru.** Sai daya daga cikinsu, ya ce, begenmu yana ga jinkan Allah da alherinsa kadai. Sai na ce, haka yake, sai mu gode wa Allah domin shi mai jinkai ne mai alheri kuma. Amma duk da haka jinkansa bai ci karo da Tsarkinsa da adalcinsa ba. Daga nan, sai daya abokin ya ce, na sani Allah zai iya yin komai, amma ka bayyana yadda Allah zai aiwatar da adalcinsa tare da nuna jinkai a lokaci guda. Sai na amsa na ce, ga mutane, wannan ba mai yiwuwa bane, idan alkali bai hukunta mai laifi ba, ya nuna jinkai, amma bai yi adalci ba. Idan ya nuna cikakken adalci, to bai nuna cikakken jinkai ba. Amma zai iya nuna cikakken jinkai a lokaci guda kuma cikakken adalci. Abokaina cike da mamaki suka yi tambaya, ta yaya? Daga nan sai na ba su wani misali. Misali, ace nayi laifi, wanda hukuncinsa biyan kudi ne mai yawa, ko kuma zama a gidan (yari) kurkuku, amma sai alkalin da kansa ya biya kudin. Ashe, bai nuna jinkai da kuma adalci a lokaci guda ba? Sai dukansu suka yarda, cewa, hakika, ya nuna jinkai da kuma adalci a lokaci guda.

**Abokaina sun yi marmarin** sanin yadda Allah yayi hakan domin yan adam. Abokaina mutanen gabas, masu aminci ne wajen tattaunawa game da al'amura irin wadannan- amma wannan tattaunawar ta sa sun gane cewa, dogara ga ayyuka (kyawawa) nagari hatsari ne. ba su yi musu ba

cewa su masu zunubi ne, yanzu suna marmarin su san yadda za su sami ceto.

**Littafi yayi bayani.** ”Tunda yake an kaddara wa dan adam ya mutu sau daya ne, bayan haka kuma sai shari'a" (Ibraniyawa 9:27). Sai na bayyana musu cewa, hukuncin zunubi mutuwa ce ta har abada – ba mutuwa ta jiki kadai ba. To, ta yaya Allah ya dauki nauyin wannan dominmu? Ta yadda ya zama (dan adam) mutum. Wannan shine ainihin abin da Almasihu yayi dominmu. Littafi Mai Tsarki ya gaya mana yadda Allah ya kaunaci yan adam kwarai. Ya aiko da Almasihu ya mutu dominmu. Almasihu da yardarsa ya mutu a madadinmu, domin duk wanda ya gaskanta da shi, kada ya hallaka, sai dai ya sami rai madawwami. Game da Almasihu kuma, Littafi Mai Tsarki ya ce, "shine duk Annabawa suka yi wa shaida, cewa albarkacin sunansa duk mai gaskantawa da shi zai sami gafarar zunubai" (Ayyukan Manzanni 10:43).

---

Akwai yan littatafai masu dauke da koyarwar Littafi Mai Tsarki da kuma shawarwari kyauta a yalwace. Idan akwai bukata, sai a rubuta zuwa ga wannan adireshi dake kasa:

Hausa-8 "The Weight Of Sin"

Free tracts and biblical counsel available by request. Write:
**Word Of Truth,** P.O. Box 1126, Kaduna, Nigeria.
PRINTED IN USA